**KOMAI NISAN JIFA III**

**EPISODE 13**

**<u>CHARACTERS</u>**

*Husseini*

*Alhaji Bature*

*Hassan*

*Jummai*

*Laraba*

*Dr. Daoud*

**EPISODE 13, SCENE 1**

**Northern Kaduna. Husseini's Shop At The Motor Park. Afternoon**

1. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**
2. **SFX:** **<u>AMBIENCE OF MOTOR PARK. HEAVY TRAFFIC. INDIAN MUSIC BLARING FROM A NEARBY SHOP.</u>**
3. **ALHAJI B:** **(COMING ON MIC)** Ina yini Husseini!
4. **HUSSEINI:** **(WELCOMING PROFUSELY)** Oh Alhaji Bature, barka da rana yalla*b*ai! Bari na *k*ara yin maka barkan auren da kayi yallabai.
5. **ALHAJI B:** Na gode Husseini....
6. **HUSSEINI:** **(CUTTING IN)** Alhaji, ina fatan kayi tafiya lafiya. Na biya ku*d*in watan ma *d*an-uwanka kamar yadda ka umurceni nayi.
7. **ALHAJI B:** **(DETACHED)** Na gode Husseni. **(FOCUSED)** Amma akwai magana da zan yi da kai.

8. **HUSSEINI:** **(NERVOUSLY)** Toh Alhaji. Ina fatan ba laifi bane nayi. Na..

9. **ALHAJI B :** (**CUTTING IN)** Baka yi laifi ba amma akwai wani abun da ya kamata kayi domin *k*arfafa dangantakarmu.

10. **HUSSEINI :** Babu damuwa, ina da shirin yin duk abun da zai *k*arfafa dangantakarmu. Kayi mun kirki sosai kuma ina matu*k*ar godiyar komai da kake ta yi mini.

11. **ALHAJI B :** Yana da kyau, shi yasa zaka yi wani abu game da abun da zan gaya maka.

12. **HUSSEINI :** Ka gaya mun Alhaji Bature, don Allah, zan yi shi. Ina mai maka biyayya, kuma a shirye nake.

13. **ALHAJI B :** Gaskiya ne wai *d*an-uwanka na takarar wata matsayi a siyasa?

14. **HUSSEINI :** (**EXCITEDLY)** Eh Alhaji, gaskiya ne. Hassan na da goyon bayan *K*ungiyan 'Yan-kasuwa a inda yake da shagon *d*inki.

15. **ALHAJI B :** **(WITH A TONE OF FINALITY)** Wannan abun takaici ne Husseini!

16. **HUSSEINI :** **(SURPRISED)** Abun takaici? Alhaji Bature, meyasa ka ce haka?

17. **ALHAJI :** Saboda ina da *d*an takaran da na za*b*a ma wannan matsayin.

18. **HUSSEINI :** Amma Alhaji, wannan abun *k*uri'a ce, sai wanda musu jefa *k*uri'a suka za*b*a zai ci nasara.

19. **ALHAJI B :** **(WITH AUTHORITY)** Kaga nine mai na*d*a sarakai a wannan garin. Ko da za'a yi za*b*e, ni nake fa*d*in wa zai hau takaran wannan matsayin.

20. **HUSSEINI :** **(IN A SUBDUED TONE)** Na gane Alhaji.

21. **ALHAJI B :** Kalli nan Husseini, bazai yi kyau *d*an-uwanka ya ja dani akan wannan matsayi bayan kowa ya san ni da kai na kusa.

22. **HUSSEINI :** Na gane Alhaji Bature. Ma kake so nayi?

23. **ALHAJI B :** Ka yi wa *d*an-uwanka magana, ka gaya mishi ya manta da yin takaran wannan matsayin domin ina da wanda nake so ya hau.

24. **HUSSEINI :** Idan *d*an-uwana Hassan yayi niyyar yin wani abu, da wuya a canza masa ra'ayi.

25. **ALHAJI B :** Sai ka sa shi ya manta da wannan. Sai dai in baka son mu cigaba da abutanmu.

26. **HUSSEINI :** Kar ka damu Alhaji. Zan yi wa Hassan magana.

27. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC.**

**EPISODE 13, SCENE 2**

**Northern Kaduna. Hajiya Innas House. Hassan And Jummai's Room.**

28. **SFX:** **TV IS ON. SOUND OF PLATES. BEING OPENED AND CLOSED. WATER IS POURED.**

29. **JUMMAI:** Maigida, na gama girki. Abincin da kafi so ne. Tuwon dawa da miyan kuka.

30. **SFX:** **WASHING HANDS. FOOD IS TASTED.**

31. **HASSAN:** Mmmm. Akwai da*d*i Jummai. Na gode.

32. **JUMMAI:** **(HAPPY)** Ina murna yayi maka da*d*i Hassan. Sai da na *k*ara man shanu domin na san kana son sa sosai.

33. **SFX:** **SOUND OF LICKING HIS FINGERS.**

34. **HASSAN:** Na gani ai. Na gode matata. Ina jin da*d*in dawowa gida domin kina da *k*o*k*ari a wajen kula da ni, kuma kina kwantar mun da hankali na.

35. **JUMMAI:** Na gode maidiga. Ina jin da*d*in zaman aure tare da kai, kuma ina son na ga farantad da kai. Kaima kana *k*o*k*ari wajen sa mun jin da*d*i ai.

36. **HASSAN:** Toh, menene labari yau Jummai?

37. **JUMMAI:** Komai lafiya. Amma sai da na tsaya wa Kande saboda tayi tafiya, ta je biki a *k*auyensu.

38. **HASSAN:** Wato yau aiki ya kama ki kenan? Gaskiya abincin ma ya fi mun da*d*i yanzu.

39. **JUMMAI:** **(LAUGHS)** Kai fa Hassan? Yaya kamfen naka ke tafiya?

40. **HASSAN:** Komai daidai yake. Ina ta samun gogyon baya daga 'yan jam'iyyarmu.

41. **JUMMAI:** **(IMPRESSED)** Daga jam'iyyar shi kansa? Haka na da kyau sosai ko*?*

42. **HASSAN:** Eh. Kaman shugabannin jam'iyyar sun gane cewa goyon bayan da *K*ungiyar 'Yan-kasuwa da sauran *k*ungiyoyi ke bani na da *k*arfi sosai.

43. **JUMMAI:** Kana ganin kaman zaka ci za*b*en?

44. **HASSAN:** Ban dai sani ba Jummai. Sai mutane sun jefa *k*uri'a za'a san wanda ya ci za*b*en.

45. **JUMMAI:** Ban da wata damuwa mai gida. Ina da tabbas a gera ka.

46. **HASSAN:** Na gode matata ma wannan goyon bayan da yarda da kike bani. Ina son na ga na taimaka wa al'umma, kuma na san zan iya yi In-sha-Allahu.

47. **JUMMAI:** Amin. Na san zaka samu nasara Hassan.

48. **HASSAN:** Ina jin da*d*i da kike tunani haka. Amma mu bar maganar siyasa. Ki matso, na zo gida ne domin na baki lokaci na ba don mu tattauna siyasa bane.

49. **JUMMAI:** **(GIGGLING LIKE A SCHOOL GIRL)** Mai gida na kenan!

50. **HASSAN:** Yaya kike ji da hanyar tazzaran ta robar hannu da muka koma kai bayan barin alura?

51. **JUMMAI:** Sun yi daidai. Kuma ina jin da*d*in cewa nan da shekara uku bazan damu da sakewa ba kamar yadda na tayi da alurar.

52. **HASSAN:** Wannan gagarumin abu ne fa. Kuma a duk lokacin da kike da bu*k*atar *d*aukar ciki sai kawai ki je asibiti a cire.

53. **JUMMAI:** Yana da sau*k*i, babu wata damuwa, kuma baya jawo wata matsala. Kana iya bada tazzara tsakanin haihuwa-da-haihuwa kamar yadda kake so.

54. **HASSAN:** **(AMOROUSLY)** Eh, muna iya yin harkar mu ba tare da dakatawa ba. **(LAUGHS)** Matso kusa matata.

55. **JUMMAI:** **(GIGGLES SHYLY)** Hassan, na san wannan muryar. Bari na kwashe kwanukan saboda ka samu ka sake jiki.

56. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**EPISODE 13, SCENE 3**

**Northern Kaduna. Outside Hajiya Innas House. Early Evening**

57. **SFX:** **<u>LIGHT TRAFFIC NOISE. CRICKETS CHIRPING</u>**

58. **DAOUD:** Na gode Laraba da kika fito kika same ni.

59. **LARABA:** (**SOFTLY)** Ba komai Daoud. Na yi mamaki da aka gaya mun wai ka zo, musamman don baka asibiti cikin wannan sati kaman yadda ka saba.

60. **DAOUD:** Eh, nayi tafiya zuwa konfarens ne, kuma bazan iya jira har sai sati mai zuwa na ganki ba, shi yasa na ce bari naga ko zan samu sa'a na zo mazaunarki.

61. **LARABA:** Toh. Na *d*an damu da ban ganka ranar Talata ba Daoud, sai da wani likita ya tsaya maka.

62. **DAOUD:** **(TEASING)** Ina farin ciki da na zo nan yau Laraba. Daga farko kin yarda kin fara kira na da sunana, na biyu kuma kin shaida mun kina tunani na.

63. **LARABA:** A’a, bana tunaninka Daoud. Amma ina da tambaya.

64. **DAOUD:** Menene tambayarki? Zaki iya mun kowacce tambaya.

65. **LARABA:** Don Allah Daoud, kana da wata dangantaka da Nas Maria? Kayi mata al*k*awarin aure?

66. **DAOUD:** **(SURPRISED)** Auren Nas Maria? A’a! Wa ya gaya miki wannan *k*aryan?

67. **LARABA:** **(EMBARRASSED)** Ni fa bana son na jawo wata fitina, amma Nas Maria tazo tayi mun garga*d*in cewa kai nata ne.

68. **DAOUD:** **(SHOCKED)** Kalli nan Laraba, ko dai tana hauka ne, ko kuma baki gane ta bane! Tun lokacin da matata ta rasu shekaru biyar da suka wuce, ban kalli wata mace ba sai ke.

69. **LARABA:** Toh Daoud, tana gani kaman akwai abu tsakaninku fa.

70. **DAOUD:** **(VEHEMENTLY)** Laraba, gaskiya, zan iya ranstewa, ba’a ta*b*a samun wani abu tsakanin ni da Nas Maria face aikinmu. Ban ma san wani abu a gare ta ba.

71. **LARABA:** Toh Daoud, na yarda.

72. **DAOUD:** Amma kin yarda da son da nake yi miki Laraba. Ba wasa nake ba fa, ina ma son na gana da iyalinki … iyali na sun riga sun san batun ki.

73. **LARABA:** **(TEASING)** Daoud, yaya ka gaya musu kafin na amince?

74. **DAOUD:** **(LAUGHS)** *K*ila bai dace ba. Amma tun lokacin dana ganki na san cewa kin dace dani. Ban ta*b*a tsammani wai zan sake soyayya. Bayan sha’awar da naji, sai halinki da kuzarinki wajen taimikon mutane ya *k*ara jawo zuciyata kusa dake.

75. **LARABA:** Eh Daoud, kuzarinka da yadda kake dagewa bisa ga *k*a'ida akan aikinka a cikin al'umma abubuwa ne da nima nake so da kai.

76. **DAOUD:** Na ga kina son karatu kema. Ina ganin kina karatu a lokacin da baki da aikin yi. Nima ina son karatu Laraba.

77. **LARABA:** **(LOOSENING UP)** Ashe kana son karatu kaima? Yana da kyau sosai. Ashe muna da abubuwa dayawa da suke daidai da juna.

78. **DAOUD:** Toh Laraba, ki gaya mun labarin iyalinki da yadda kika girma.

79. **LARABA:** **(CLAMMING UP)** Erm, tarihi na ba wani abu bane, bari naji naka.

80. **DAOUD:** **(SUSPICIOUS)** Amma na sha gaya miki labarin iyali na. Yaya kika ja da baya da na tambaye ki batun iyalinki?

81. **LARABA:** **(NERVOUS)** Daoud, ya kamata na shiga ciki yanzu. Sauro yayi yawa a nan waje.

82. **DAOUD:** Kalli nan Laraba, ina *d*aukar wannan soyayya da muhimmanci fa. Yaushe zaki sake jiki ki gaya mun labarinki ne?

83. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**EPISODE 13, SCENE 4**

**NORTHERN KADUNA. HAJIYA INNA'S RESIDENCE. NIGHT.**

84. **SFX:** **<u>KNOCK ON THE DOOR FOLLOWED BY SOUND OF DOOR OPENING</u>**

85. **HUSSEINI:** Hassan! Yaya kake?

86. **HASSAN:** **(WARMLY)** Husseini! Barka da zuwa. Yaya kake? Yaya kasuwa?

87. **HUSSEINI:** Kasuwa Alhamdulillah. Alhaji Bature yana ta yi mini kirki.

88. **HASSAN:** Ina farin ciki da muka samu mutum mai hankali da taimako kamar Alhaji Bature a wannan gari.

89. **HUSSEINI:** **(NERVOUSLY)** Toh Hassan, *d*an-uwa na, yaya kamfen naka yake gudana?

90. **HASSAN:** **(EXCITEDLY)** Yana tafiya daidai sosai Husseini. Na gode da *k*arfin gwiwan da ka bani na taya wannan za*b*en. Ba don kai ba, da ban yi ba.

91. **HUSSEINI:** **(SIGHS DEEPLY)** Hmm!

92. **HASSAN:** (**SURPRISED)** Menene kuma? Ko baka taya ni murna ne Husseini?

93. **HUSSEINI:** Yaya bazan tayaka murna ba Hassan? Kai *d*an-uwana ne! sai dai …

94. **HASSAN:** **(CUTTING IN)** Menene?

95. **HUSSEINI:** **(DRAWS A DEEP BREATH)** Alhaji Bature ya zo shago na yau ya gaya mun cewa shine mai na*d*a sarakai a wannan garin.

96. **HASSAN:** Mai na*d*a sarakai? Me ya ha*d*a na*d*in sarki da kamfen na kuma?

97. **HUSSEINI:** A *k*alla Alhaji Bature yana ganin cewa wannan matsayin da kake nema na wani nashi ne.

98. **HASSAN:** Amma jam'iyyarmu ba *d*aya bane. Idan Alhaji shine mai na*d*a sarakai ai sai ya maida hankali akan *d*an takaran jam'iyyarsa.

99. **HUSSEINI:** Abun da na gaya masa kenan amma ya dage da cewa sai na zo na gaya maka.

100. **HASSAN:** Me yake fatan gaya mun zai sa Husseini?

101. **HUSSEINI:** **(NERVOUSLY)** Toh Hassan, yana so ka ja baya, ka ba wa nashi *d*an takaran dama.

102. **HASSAN:** **(WITH SOME FORCE)** Wannan ba zai yu ba! Bazan yi haka ba!

103. **HUSSEINI:** **(PLEADING)** Hassan Alhaji ya nuna cewa idan ka nemi wannan matsayin zai janye taimakon da yake mini. Hassan ka san iyalina na dangana da taimakonsa …

104. **HASSAN:** Amma wannan sharri ne ai! bai dace ba ko ka*d*an. Na zubar da maganar da nayi a baya wai shi mutumin kirki ne.

105. **HUSSEINI:** **(HOPEFUL)** Toh Hassan, zaka janye daga za*b*en?

106. **HASSAN:** Bazan janye ba. Idan Alhaji Bature na tunanin cewa matsayin na mutuminsa ne, toh ya jira ayi za*b*e a ga wanda masu jefa *k*uri'a zasu za*b*a!

107. **HUSSEINI:** Hassan, hukuncin da ka yanka kenan? Baza kayi nazari ba?

108. **HASSAN:** Husseini, don Allah kar ka tambaye ni nayi wannan. A bar mutane su yi za*b*insu!

109. **<u>THEME MUSIC AND END CREDITS</u>**